## Ko Kana Da Kyau, Ka Qara Da Wanka: Alfanun Koyar Da Sana'o'in Gargajiya Na Hausawa a Makarantunmu

**Sama'ila Mohammed**
samailadtm@gamail.com
07030380456
Sashen Nazarin Harshen Hausa, Kwalejin Ilimi Da Koyan Aikin Shari'a Ta Dakta Yusuf Bala Usman Da Ke Daura

**Tsakure**

Sana'o'in Hausawa na gargajiya suna xaya daga cikin vangaren ci gaban tattalin arziqin Hausawa a qasar Hausa baki xaya.Ganin irin alfanun da sana'o'in Hausawa na gargajiya kamar qira da sassaqa da fawa da saqa da rini da wanzanci da noma da jima da gini da dukanci, suke da su, ta fannin samar da ayyukan yi da kuma magance zaman banza a tsakanin al'umma da kuma gina tarbiyya da raya al'adun Hausawa. Wannan bincike ya yi tsokaci a kan alfanun cusa ilimin koyar da sana'o'in Hausawa na garagajiya a makarantun gaba da sakandire, haka kuma binciken ya fito da alfanu tare da asalin samuwar sana'o'in Hausawa na gargajiya da kuma ire-iren sana'o'in gargajiya kamar yadda masana da manazarta suka fitar da su. Kazalika an kawo bayanai na irin yadda waxannan sana'o'in suke taka muhimmiyar rawa wajen kare xalibai daga faxa ma wasu munanan halaye masu ruguza rayuwarsu. Bugu da qari sana'o'in gargajiyar suna samar masu da abubuwan tafiyar da rayuwar cikin sauqi, ba tare da wasu matsaloli ba. Haka kuma, akwai tsokaci a kan ma'anar sana'a da ma'anar koyarwa da kuma bayanai a kan alfanun koyar da sana'o'in Hausawa na gargajiya. Sannan an kawo ra'in da aka yi amfani da shi domin xora binciken a kai.

### 1.0 Gabatarwa

Hausawa na cewa "Sana'a sa'a rashin sana'a sata" kuma sana'a goma maganin mai gasa. Sana'o'in gargajiya na Hausawa, sana'o'i ne da aka gada tun iyaye da kakanni ake aiwatar da su a qasar Hausa, kuma suna da matukar alfanu ga rayuwar al'ummar Hausawa. Sana'o'in sun shafi dukkan tafarkin rayuwar da mutum kan zava a matsayin madogararsa ta rayuwar yau da kullun.

A gargajiyence, sana'o'in gargajiya suna da daxaxxen tarihi a qasar Hausa, an ce sana'ar farko ita ce farauta kuma ita ce aka fara gudanarwa a qasar Hausa (Ado, 2014). Sana'a aba ce da ta shafi gado, wato tun iyaye da kakanni, kuma sana'a wata hanyar rayuwa ce da xan adam kan dogara da ita domin samun abin masarufi (Sulaiman, 2007). A gargajiyence, sana'a ita ce ta farkin da Bahaushe kan bi domin samun abububwan da yake buqata, ta hanyar sarrafa albarkatun qasa (Alhassan, 1988).

A ra'ayin mai bincike kuwa Sana'a ita ce hanya wadda mutum zai riqe domin dogaro da kai da kuma samun rufin asiri da zamantakewa mai xorewa a cikin al'ummar da suke cuxanya tare da juna.

A wannan bincike an yi qoqarin fito da kaxan daga cikin alfanun cusa ilimin koyar da sana'o'in Hausawa na gargajiya a makarantun gaba da sakandare domin fito da abubuwan da bincike ya tabbatar da su. Ana sa ran hakan, masana da manazarta za su fahinci wasu fa'idoji na cusa koyar da sana'o'in gargajiya ga xaliban makarantun gaba da sakandire a qasar Hausa domin samun madogara a rayuwa.

## 2.0 Asalin Sana'a

Hasawa na cewa, "tun kafin a haifi uwar mai sabulu balbela take da farinta". Abin nufi shi ne, "tun ran gini, ran zane", wato tun fil'azal aka ga Hausawa da sana'o'insu na gargajiya. Kenan, a tarihi babu wani ko wata qabila ko al'umma da ta sa Hausawa a gaba ta koya masu yadda ake yin sana'o'i. Tun asalin kafuwar zaman Hausawa a farfajiyar da ake kira "qasar Hausa", suka tashi da iya sarrafa albarkatun da Allah ya halitta a kewaye da su, suna biyan buqatunsu, na rayuwar yau da kullum.

Kamar yadda kowace al'umma ta duniya ta fara gudanar da sana'o'in gargajiya, haka ma Hausawa sun fara yin sana'o'in ne domin neman biyan buqatun rayuwarsu ta abinci (Yahaya,1992). Sana'ar farauta ita ce babbar dabara ta farko da Bahause ya fara yi a lokacin da ya zo qasar Hausa (Ado, 2014, Alhassan, 1988).

Baya ga sana'ar farauta, wata sana'ar da Hausawa suka tsiri yi ita ce sana'ar gardanci, kiwo da qira da sassaqa da noma da rini da saqa da jima da fawa da dukanci da gini da wanzanci da sauran makamantansu (Alhassan 1988). Idan aka lura da waxannan bayanai, za a ga cewa, tun farkon zuwan Hausawa a farfajiyar qasar Hausa suke yin sana'o'in gargajiya daban-daban kama daga sana'ar farauta har zuwa sauran sana'o'in gargajiya iri daban-daban a qasar ta Hausa. Kuma duk suna gudanar da su ne domin samun madogara a rayuwarsu ta yau da kullum.

## 2.1 Ma'anar Sana'a

Masana da manazarta a fagen ilimi, sun fitar da ma'anar sana'a ta hanyar kalamai iri daban-daban. Sana'a wata hanya ce ta amfani da azanci da hikima a sarrafa albarkatu da ni'imomi da xan adam ya mallaka domin biyan bukatu na yau da kullum (Yahaya, 1992). Sana'a wata hanyar rayuwa ce da xan adam ya ta'allaqa da ita domin samun abun masarufi (Sulaiman, 2007).

Sana'a al'amari ne da ya shafi wani ta farkin rayuwar da mutum kan zava ya riqa aiwatar da ita domin samun hanyar biyan buqatun rayuwarsa, kuma sana'a wani batu ne da ya shafi gado wato aka gada tun iyaye da kakanni (Auta,2002). Sana'a wata aba ce mai matsayi a wajen Hausawa, domin hanya ce ta dogaro da kai da kuma samun abubuwan buqata na rayuwar yau da kullum (NNPC,1968).

A ra ayin mai bincike, sana'a wata hanya ce wadda mutum kan zava ko ya gada, ya riqayi domin dogaro da kai ko samun abin masarufi na yau da kullum.

## 2.2 Ire-iren Sana'o'in Hausawa Na Gargajiya

Sana'o'in Hausawa na gargajiya sun kasu kashi uku, akwai na maza da na mata da kuma waxanda suka yi tarayya, wanda kowane kashi yana xauke da nasa vangaren, wanda za a iya ganin su da bayanin su a taqaice kamar haka:

**1.Sana'o'in Maza**
Irin waxannan sana'o'in su ne waxanda maza ke gudanar da su, domin da wuya a samu mace ko mata na gudanar da su. Misali waxannan sana'o'I su ne:
Farauta da Gini da Wanzanci da Jima da Rini da Qira da Su (kamun kifi) da sauransu. (Alhassan, 1988).

1. **Sana'o'in Mata**
Irin waxannan sana'o'i su ne waxanda suka danganci mata kawai. Misalign waxannan sana'o'in akwai: Kaxi da Kitso da Sussuka da Unguwar zoma da Daka da Qunshi da kuma Tuya(Alhassan, 1988)

**3. Sana'o'in Tarayya**
Akwai sana'o'i na haxa ka ko tarayya da al'ummar Hauasawa ke gudanarwa, wato maza na yi mata ma na yi. Irin waxannan sana'o'in na tarayya su ne: Kiwo da Xinki da Roqo da Dillanci da Saqa da Waqa da Bori da kuma Bokanci (Alhassan, 1988).

**3.0 Ra'in Bincike**
Ra'in wani bayani ne na wani ilimi wanda ke nuna tsarin yadda za a xora bincike a kai. Wasu kuma na kallon sa a matsayin wani tunani ko hasashe ko bayani na ilimi wanda masana da manazarta ke amfani da shi a matsayin mizani na yin awon wasu nazarce-nazarce a faxin duniya (Gusau, 2017; Ado, 2017).

A wannan takarda, an zavi a xora ta bisa "Ra'in Alfanun sassan al'umma (functionalism theory of culture). Ra'i ne da ke bayanin alfanun a sassan al'umma ko al'ada tare da samar da cigaba a tsakanin al'umma ta fuskar zamantakewa. Wannan ra'i ne da wani Bature mai suna Charle Darwin ya qirqiro a (1985), sannan aka samu mabiya irin su Thomas Malthus da Emile Durkheim. Akwai kuma masana irin su (Ado, 2017; Gusau 2015), da suka aiki da wannan Ra'i.

Dalilin da ya sanya aka zavi wannan ra'in shi ne;
Da farko domin ra'in ya ba da haske a kan alfanun da ke tattare da sana'o'in gargajiya, tare da gyara rayuwar al'umma ta yau da kullum ta fuskar riqe sana'o'in gargajiya. Sannan ya fito da hikima da dabara da fasaha wajan gudanar da sana'o'in gargajiya na Hausawa.

To, a wannan bincike, an yi nazarin Sana'a da alfanun koyar da ita da zummar fito da alfanunta ga xalibai domin dogaro da kai, ba sai sun jira gwamnati ta ba su aiki ba.

**4.0 Ma'anar Koyarwa**
Ganin irin yadda koyarwa take da alfanu shi ya samar da wasu masana suka yi qoqari domin fitar da ma'anar koyarwa a fagen ilimi. Koyarwa wani aiki ne na hulxa tsakanin mutum da mutum domin kawo canje-canje a kan abin da mutum ya sani ko ya iya ko wanda ya yarda da shi (Zaruk, 1979).

Koyarwa wani yanayi ne da malamai kan yi amfani da wasu hikimomi na musamman domin cusa ilimi ko tunani mai kyau zuwa ga xalibai ta hanyar koyarwa, haka kuma, koyarwa wata mu'amula ce ko hulxa da ake gudanarwa a tsakanin malami da xalibai da nufin canja halaye ko xabi'un mai koyo su zama masu kyau (Fafunwa, 2002).
A bisa al'akari da ma'anar koyarwa, a iya cewa hulxa ce tsakanin malami da almajiri ko xalibai domin isar da saqo da nufin samar da canje-canje da cigaba a cikin al'umma.

## 4.1 Alfanun Koyar da Sana'o'in Gargajiya ga Xaliban Makarantun Gaba da Sakandire

Alfanu dai a taqaice na nufin moriyar wani abu a cikin al'umma, sabada haka koyar da sana'o'in gargajiya ga xaliban makarantun gaba da sakandare a qasar Hausa abu ne mai mutuqar alfanun wanda ba ya misaltuwa da kuma iyakancewa a cikin al'umma. (Madauci, 1980).

Wannan binciken ya tabbatar da cewa wasu qasashen duniya da suka ci gaba irin su qasar Sin da Japan da Taiwan da korea, sun samu cigaba ne ta fuskar dogara da sana'o'i wato qere-qere. Misali a qasar Sin da Japan xaliban firamare da sakandire su ne suke samar da agoguna da fitilun samar da haske qanana da kuma rediyo qanana da sauran su. A India kuwa, xaliban sakandire ne ke samar da qanana kayan da ake amfani da su a gonaki irin su fartanya da gatari da lauzuna da wuqaqe da sauran wasu kayan ma'aikaci a gida. Babu shakka, wannan turba ta ilimin xalibai ta haifar wa qasashe cigaba na musamman da kuma kare su daga faxawa mummunan xabi'u waxanda duniya ke qyama. (Abdu, 2006).

A bisa wannan dalili ne wannan bincike ya fito da wasu alfanu ko fa'idojin koyar da sana'o'in gargajiya na Hausawa a makarantun gaba da sakandire na qasar Hausa. Domin kuwa, a yau an wayi gari ya'yan Hausawa suna da qarancin ayyukan yi da zaman kashe wando, da kuma cusa kai cikin qungiyoyi na banza da shiga bangar siyasa, musamman a wannan lokaci na guguwar siyasa. Kaxan daga cikin alfanun da fa'idojin koyar da sana'o'in Hausawa na gargajiya sun haxa da samar da ayyukan yi, saboda tun da farko iyaye ke koyar da 'ya'yansu sana'ar gida, hakan ba zai wadatar ba a yau, har sai an haxa da koyar da sana'o'in gargajiya a harkar koyarwa a makarantun gaba da sakandare musamman a wannan lokaci da shirin game duniya (Globalization) ya mamaye duniya ta hanyar sadarwa da yaxa manufofi a kan tallata sana'o'i a faxin duniya.

Bagu da qari, irin sana'o'in gargajiya da yakamata a inganta su akwai sana'ar qira da rini da jima da noma da saqa da fawa da gini, da kafinta wanda yin haka zai haifar wa sana'o'in kwarjini da ban shi'awa a idon duniya, wanda zai sa a samu wasu su riqa alfahari da sana'o'in har a kai ga an magance zaman banza da rage yi ma gwamnatoci zuru idan an kamala karatu.

### 4.1.1 Bunqasar Tattalin Arziqi

Wannan wani vangare ne da ke da alfanu a tattare da koyar da sana'o'in gargajiya na Hausawa ga xaliban makarantun gaba da sakandire. Misali, ganin yadda halin rayuwa yake a yau a cikin al'ummar Hausawa na tavarvarewar tattalin arziki, idan xalibai suka koyi sana'o'i za su samu madogara sannan kuma a samar da kuxaxen shiga.

**4.1.2 Raya Al'adun Gargajiya**

Al'ada aba ce wadda ta mamaye rayuwar Bahaushe, domin kuwa yana al'fahari da al'adunsa. Koyar da sana'o'in Hausawa na gargajiya a makarantun gaba da sakandire ga xalibai za ya taimaka wajan sanin al'adun kowace sana'a. misali a sana'ar qiran zabira, ta zo da kanta, akwai kuma al'adar yi ma tulu qaho har a fitar da jini. Haka ma, al'adar hawan qaho ga masu sana'ar fawa da al'adar baqar magana.

**4.1.3 Koyar Da Tarbiyya**

Kamar yadda sana'o'in gargajiya na Hausawa, kamar su qira da fawa da rini da wanzanci da xori suke da matuqar muhimmanci a zamantakewar al'ummar Hausawa, kuma suka zama abin dogaro da kai, ya sa ake samun tarbiya mai mutuqar alfanu da fa'idoji ga kowace al'umma, saboda haka, koyar da sana'o'in gargajiya ga xaliban makarantun gaba da sakandire kan taimaka qwarai wajen rage yawan rashin tarbiyya a yau, hanyar koyar da sana'o'i ita ce ke nuna ma mai koyo yadda zai yi biyayya ga na gaba da shi, kuma wannan biyayyar ita ce zata taimake shi ya samu xaukaka a fagen sana'ar da ya koya a gida ko a cikin alumma.

**4.1.4 Samar Da Abubuwa Na Musamman**

Mahimmancin sana'o'in gargajiya na Hausawa, yana haifar da abubuwa na musamman, idan muka kalli sana'ar fawa da jima suna samar da abubuwan amfani ta hanyar fatu. Sannan kuma, idan aka kalli sana'ar qira takan samar da kayan aikace-aikacen gida da gona da kayan faxa ko makaman yaqi. Ta hanyar koyar da sana'o'in Hausawa na gargajiya a makarantun gaba da sakandare, kan haifar da samuwar waxansu abubuwa na rayuwa. Misali idan aka xauki sana'ar jima da qira aka kuma ba su mahimmanci, za'a samu abubuwa kamar takalma da jaka da buzun sallah a vangaren jima. A vangaren qira kuwa, za a samu kayan ma'aikaci kamar su fartanya, shebur, diga da sauransu.

**4.1.5 Samar Da Aiyukan Yi**

A zamantakewar al'umma a yau, za mu ga cewa aiyukan yi sun yi qaranci a tsakanin al'umma musamman ma ga matasa. Ta hanyar koyar da sana'o'in gargajiya da ba su mahimmanci, zai taimaka a samu ayyukan yi a cikin al'umma da rage zaman banza da shiga bangar siyasa musamman ma xalibai masu tasowa, da kuma rage yi wa gwamnatoci zuru su samar da ayyukan yi bayan kammala karatu.

**5.0 Shawarwari**

Tabbas sana'o'in Hausawa na gargajiya abu ne masu faxin gaske waxanda ke buqatar taimako daga masu nazari domin su havvaka su daga gargajiya zuwa na zamani. Amma duk da haka, ana buqatar tallafi daga waxanda suka gaji sana'o'in, wato masu sanao'in gado. Saboda haka ne aka kawo waxannan shawarwari.

- **Shigowar qungiyoyin Iyaye da malamai:** ya kamata, waxannan qungiyoyin su haxa qarfi da qarfe domin tallafawa xaliban makarantun gaba da sakandire wajen koyar da sana'o'in gargajiya domin su samu dogaro da kansu.
- **Shigowar hukumomi:** A wannan vangare yana da kyau hukumomin ilimi su shigo da tsarin koyar da sana'o'in gargajiya a zamanance domin havvaka su, su zama abin shi'awa ga kowa da kuma qima a idon duniya, da magance zaman banza a tsakanin al'umma.

- **Shigowar masu hannu da shuni:** A wannan vangaren ya kamata masu hannu da shuni su taimaka wajen gina masana'antu irin na sana'o'in gargajiya domin tallafawa al'umma masamman matasa su rage yi ma gwamnatoci zuru wajen jiran ayyukan yi.
- **Shigowar sarakuna:** Su ma sarakuna ba a bar su a baya ba, a matsayinsu na iyayen qasa, ya kamata su riqa shirya taruka domin ilimintar da al'umma musamman matasa a kan muhimmancin sana'o'in Hausawa na gargajiya waxanda aka gada tun iyaye da kakanni don dogaro da kai.

## 6.0 Kammalawa

Sana'o'in na gargajiya, sana'o'i ne da suke da matuqar alfanu da fa'idoji da kuma kawo sauyi da ci gaba a qasar Hausa baki xaya. Haka kuma, nazarin inganta sana'o'in gargajiya zuwa na zamani zai haifar da gagarumin cigaba ga rayuwar xalibai baki xaya a qasar Hausa. Sannan kuma, za a samar da aiyukan yi wanda za ya hana zaman banza a tsakanin al'umma musamman ma matasa tasowa a qasar Hausa.

## Manazarta


Abdu D.M (2006). *Tasirin kimiyya da qere-qeren zamani kan sana'o'in Hausawa na gargajiya.* Zaria: N.N.P.C Press.

Ado, A. (2014). *Sana'ar Gardancin Hausawa, Asalinta da yadda take da yadda Ake Yin ta a Qasar Hausa*. Cairo, Egypt: Al-adab 42 opera square.

Ado, A. (2017). *Ra'o'in Bincike kan Al'adun Hausawa*. Katsina: Kanki classical Media Enterprises.

Alhassan, H. da Musa, U.I da Zuruk, R.M. (1988). *Zaman Hausawa, Bugu na biyu.* Lagos: Islamic publition Bureau.

Auta, A.L. (2002). *Sana'o'in Gargajiya na Hausawa.* Unpublished article.

Babs, A.F. (2002). *History of Education*. Ibadan: University press plc.

Gusau, S.M. (2015). *Mazhabobin Ra'i da Tarke a Adabi da Al'adu na Hausawa.* Kano: Century Research and publishing limited.

Madauci da wasu, (1980). *Hausa Customs.* Zaria: N.N.P.C Press.

Muhammad, R.Z. (1979). *Siffofin Aikin Koyarwa.* Ibadan: Oxford University Press.

Northern Nigerian Publishing Company (1969). *Labaru Na Da naYanzu*. Zaria: NNPC Printing Press.